Manzon Allah ya Kasance yana hadawa a tafiya tsakanin Azahar da La'asar; idan ya kasance akan abin hawa, kuma yana hadawa tsakanin Magriba da Isha.

Daga Abdullahi dan Abbas ya ce: "Manzon Allah ya Kasance yana hadawa a tafiya tsakanin Azahar da La'asar; idan ya kasance akan abin hawa, kuma yana hadawa tsakanin Magriba da Isha"

[Ingantacce ne] [Buhari ne ya rawaito shi]

Shari'ar Annabi Muhammadu tayi Daban da sauran Shari'u da aka saukar daga sama wajensauki da kuma kawar da duk abinda zai jawo takura ko Matsuwa ga barin bayi ko kuma ta saukake musu shi, daga cikin wadan nan saukin hada salloli biyu lokacin tafiya wadanda suke da tarayya a lokaci, sabida Asali wajabcin yin kowace daya a lokacinta, saidai da ya kasance yana daga Al'adar Annabi idan yayi tafiya kuma tafiyar tai tafiyayakan hada tsakanin Azahar da La'asar, kodai a farkon lokaci ko kuma a karshen lokaci, haka kuma yana hana hada Magriba da Isha kodai Jam'i a farko ko kuma a karshe kuma yana a cikin hakan wanne ne yafi masa sauki acikinsu da wadanda suke tare da shi, sai ya kasance tafiyar tasa ita ta janyo hadawar a lokacin daya daga cikin biyun kuma lokacin

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5323